Jerin Littafan Shi’a Na 8

# Mugun Nufin

# ‘Yan Shi’a

# ga

# Al’umma

Umar Labɗo

# بسم الله الرحمن الرحيم

## Gabatarwa

'Yan Shi'a suna da baƙin tarihi wanda yake cike da ta'addanci da rura wutar fitina tsakanin Musulmi da taimakon kafirai a kansu wajen yaƙar su da cinye ƙasashensu, domin su, kamar yadda Ibnu Taimiya yake faɗi, "A koda yaushe suna neman taimako da kafirai da fajirai wajen biyan buƙatunsu kamar yadda suke taimakon kafirai da fajirai wajen biyan nasu buƙatun."[1] Wannan shi ne halin Rafilawa a tsawon tarihinsu, a ko wane zamani, kuma a ko wane wuri.

A nan Nijeriya, an ruwaito madugunsu, Ibrahim Yaƙub Alzakzaki, yana faɗa wa Kiristoci, waɗanda yake gayyata wajen Maulidinsa: "Ba da ku muke faɗa ba," yana nufin su da Musulmi suke yaƙi; ba da kafirai ba. Su kafirai abokan tafiya ne; saboda haka Kiristoci suke halartar Maulidin 'yan Shi'a, inda suke ɗaga Kuros, watau suna nuna alamar addininsu a fili ba a ɓoyewa.

Baƙin tarihin 'yan Shi'a aiwatarwa ne ga miyagun aƙidojinsu na ƙiyayya da gaba ga Ahalus Sunna, da ma duk wani Musulmi wanda ba ya bin tafarkinsu. Malaman Shi'a suna ƙoƙarin cusa gaba da ƙiyayya da mugun nufi a zukatan mabiyansu ta hanyar ruwayoyin ƙarya da suke dangana wa Imamansu, waɗanda suke nuna halaccin jinin duk wanda ba ɗan Shi'a ba,[2] da yin albishir da mummunar makomar da take jiran sa.

A wannan taƙaitaccen littafi, za mu fara da bayanin mugun nufin 'yan Shi'a ga al'umma kamar yadda yake a cikin aƙidunsu da littafan manyan malamansu. Sa'an nan daga bisani mu kawo misalai na baƙin tarihinsu wanda yake tabbatar da ƙaddamar da wannan mugun nufi a aikace.

---

[1] **Minhajus Sunna** na Ibnu Taimiyya, bugun Darul Kutubil Ilmiyya, Bairut, ba tarihi, mujalladi na 2 shafi na 195.
[2] Duba littafinmu, **Matsayin Musulmi a wajen 'Yan Shi'a.**

## Babi na Ɗaya

## Mugun Nufin 'Yan Shi'a ga Al'umma

'Yan Shi'a suna ƙudure mugun nufi ga Musulmi da Musulunci kuma wannan yana bayyana a fili daga abinda yake rubuce a cikin littafansu da abinda ke fitowa daga bakin manyan malamansu. Manufarsu ta ƙarshe ita ce ganin bayan Musulunci baki ɗayansa, da hallaka Musulmi, da rushe ɗakin Ka'aba da Masallacin Annabi na Madina, da mayar da alƙiblar Musulmi zuwa birnin Kufa. Wannan mugun nufi nasu yana bayyana a cikin aƙidarsu ta Mahadi da irin abubuwan da Mahadin nasu zai yi idan ya bayyana.

Aƙidar Mahadi a tushenta aƙida ce ta Musulunci, amma malaman Shi'a sun sauya ta, inda suka cusa ƙiyayyar Majusawan Farisa a cikinta, suka mayar da ita wani mataki na tanadin rama gayya da ɗaukar fansa a kan Larabawa (watau Sahabban Annabi) waɗanda suka rusa daular Majusawa ta Iran a zamanin Sarkin Musulmi Umar binul Khaɗɗabi, Allah ya ƙara masa yarda.

Hadisan Annabi (SAW) ingantattu masu yawa sun taho da bayanin Mahadi da sunansa da sunan mahaifinsa da sifofinsa da wurin da zai fito da lokacin da zai bayyana da kuma ayyukan da zai gabatar idan ya bayyana. Bayyanar Mahadi tana cikin alamomin ƙarshen zamani da kusantar tashin alƙiyama, kuma ƙuduri da shi ɓangare ne na aƙidojin Ahalus Sunna, saboda hadisan da suka zo da shi ingantattu, mutawatirai.

Mahadi zai bayyana a ƙarshen zamani. Zai fito daga zuri'ar Annabi (SAW), daga 'ya'yan Faɗima, Allah ya ƙara mata yarda, ta ɓangaren ɗanta Hassan (RA). Sunansa zai zama Muhammad binu Abdillah, zai bayyana daga gabashin duniya, kuma za'a yi masa mubaya'a a ɗakin Ka'aba. Zai yi mulki shekara bakwai kuma a zamaninsa Annabi Isa (AS) zai sauko zuwa duniya ya yi sallah a bayansa. Mahadi

zai cika duniya da adalci a bayan an cika ta da zalunci, zai kashe alhanzir kuma zai karya kuros. Waɗan nan abubuwa uku, watau sallar Annabi Isa a bayansa da kisan alade da karya Kuros, nuni ne ga ƙarshen addinin Kirista da shafewarsa. Wannan shi ne abinda hadisai suke tabbatar da shi dangane da al'amarin Mahadi.

Abu Sa'id Alkhudri, Allah ya ƙara masa yarda, ya ruwaito cewa Annabi (SAW) ya ce, "Mahadi daga gere ni yake, mai ƙarancin gashin goshi, mai doron hanci. Zai cika duniya da adalci bayan an cika ta da zalunci. Zai yi mulki shekara bakwai."[1] Jabir binu Abdillah, Allah ya ƙara masa yarda, ya ruwaito, ya ce: Na ji Manzon Allah (SAW) yana cewa, "Wata tawaga daga al'ummata ba za su gushe ba suna yaƙi a kan gaskiya, suna masu rinjaye, har tashin alƙiyama…Sai Isa ɗan Maryamu, tsira da aminci su tabbata a gare shi, ya sauko, sai sarkinsu ya ce: Wuce ka yi mana sallah. Sai ya ce: A'a, lallai sashenku shuwagabanni ne a kan sashe, saboda girmamawar Allah ga wanan al'umma."[2] Har yau, Abu Sa'id, Allah ya ƙara masa yarda, ya ruwaito, ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce, "Isa ɗan Maryamu zai sauko, sai Sarkin Musulmi Mahadi ya ce: Wuce ka yi mana sallah. Sai ya ce: A'a, lallai sashenku shugabannin sashe ne don girmamawar Allah ga wannan al'umma."[3]

Wannan shi ne labarin Mahadin Musulunci, da yadda zai bayyana, da yadda zai shugabanci duniya, ya shafe addinin Kirista, kuma ya kawo adalci da zaman lafiya a bayan ƙasa.

Mahadin Shi'a ya sha bamban da Mahadin Musulunci a sunansa da haihuwarsa da ayyukan da zai ƙaddamar a yayin bayyanarsa. Da farko, shi sunansa Muhammad binul Hassan Al'askari, kuma ba haihuwar sa za'a yi a nan gaba ba, a'a shi an riga an haife shi tun kimanin shekaru dubu da ɗari biyu da suka wuce. Kuma a duk tsawon waɗan nan shekaru, yana nan a ɓoye a wani kogo a birnin

[1] A duba **Sunan Abi Dawud**, *Kitabul Mahadi.*
[2] **Sahih Muslim**, *Kitabul Iman, Babu nuzuli Isa.*
[3] A duba **Almanarul Munif** na Ibnu Qayyimil Jauziyya, shafi na 147-148.

Samarra wanda a yau yake a ƙasar Iraƙi. Wannan shi ne abu na farko da ya mayar da Mahadin Shi'a almara.

Mahadin Shi'a zai fara da Larabawa, domin su ne tushen Musulunci, ya gama da su.  Muhammad Baƙir Almajalisi, ɗaya daga cikin manyan malaman Shi'a masu yawan  talifi, ya ruwaito cewa idan Mahadinsu ya bayyana zai zubar da jinin Larabawa kuma ya hakaito shi yana cewa, "Babu abinda ya rage tsakaninmu da Larabawa sai yanka."[1]

Dangane da sauran Musulmi Ahalus Sunna waɗanda ba Larabawa ba, 'yan Shi'a suna da fatawa mai ƙarfi daga imaminsu na shida Abu Abdullahi Ja'afar Sadiƙ, kan halaccin jininsu.  Wani mai ruwayarsu da ake kira Dawud binu Farƙad ya ce: Na tambayi Abu Abdillahi(A.S): Me za ka ce dangane da kisan nasibi (watau Ahalus Sunna)?  Sai ya ce, "Jininsa halal ne sai dai ina jiye maka tsoro. Idan ka samu iko ka rusa masa gini a ka, ko ka nutsar da shi a ruwa don kada a samu shaida, to ka aikata."[2]

Da yake sharhi a kan wannan ruwaya, imamin Shi'a na wannan zamani, Ayatullahi Ruhullahi Khumaini ya yi ƙari kamar haka: "Idan ka samu iko ka karɓi dukiyarsa, karɓe ta ka aiko mana da khumusi."[3]  Wannan ƙarin bayani daga Khumaini yana nuna cewa wannan aƙida ta 'yan Shi'a tana nan ba ta sauya ba; abinda kurum yake hana su aiwatar da ita shi ne rashin iko.

Wani abinda yake ƙara tabbatar da haka shi ne abinda Khumaini ya faɗa wa Sayyid Hussain Musawi a lokacin da ya ziyarce shi a birnin Teheran, bayan

---

[1] **Biharul Anwar** na Muhammad Baqir Alajalisi, bugun Muassasatul Wafa, Bairut, 1403,  mujalladi na 52  shafi na 318 da 349.
[2] **Biharul Anwar,**  mujalladi  na 27  shafi na 231.
[3] **Kashful Asrar wa Tabri'atil A'immatil Adhar** na Sayyid Hussaini Musawi, bugun Darul Iman, Iskandariyya, 2002,  shafi  na  89.

nasarar juyin juya halin ‘yan Shi’a na Iran a shekarar 1979. Musawi ya ce: A wani zama na musamman tare da Imam ya ce mini: “Sayyid Hussain, lokaci ya yi na zartar da wasiyar imamai, amincin Allah ya tabbata a gare su. Za mu zubar da jinin nasibawa (Ahalus Sunna), mu karkashe ‘ya’yansu maza, mu raya matansu. Ba za mu bar ɗaya daga cikinsu ya kuɓuta ba daga wannan uƙuba. Da sannu dukiyoyinsu za su zama ganima ga Shi’ar Ahalul Baiti. Kuma za mu shafe Makka da Madina daga doron ƙasa saboda waɗan nan birane biyu sun zama mafakar ‘yan Wahhabiya. Kuma lallai ne Karbala, ƙasar Allah mai tsarki, ta zama ita ce alƙiblar mutane a cikin sallah. Za mu tabbatar da burin imamai, aminci ya tabbata a gare su.”[1]

Kafin mu ci gaba, bari mu tuna wa mai karatu cewa, a koda yaushe ‘yan Shi’a suka ruwaito irin wannan taɓargaza suka dangana ta ga imamai, ya sani cewa imamai barrantattu ne daga wannan ƙarya wacce take nuna kafirci da munafinci da ƙin Allah da Manzonsa da Musulmi baki ɗaya. Malaman Shi’a jikokin Majusawa suna fakewa da son imamai da Ahalul Baiti, suna ɗaukar wannan a matsayin wani mayafi wanda suke lulluɓe kafircinsu da zindiƙancinsu da shi.

Amma faɗin Khumaini cewa za su rushe Makka da Madina saboda sun zama mafakar ‘yan Wahhabiya, to wannan dalili da ya bayar na rushe Ka’aba ƙarya ce kawai. Tun kafin a haifi Muhammad ɗan Abdulwahhab, ko a san Wahhabiyanci, Rafilawa suna da aƙidar rushe Ka’aba da Masallacin Annabi (SAW) na Madina.

Wani mugun nufi da ‘yan Shi’a suka daɗe da shi a zuci, kuma suke da niyar zartar da shi har gobe, shi ne rushe Masallaci mai Alfarma, watau Ɗakin Ka’aba, da Masallacin Annabi (SAW) a Madina da kuma sauya alƙiblar Musulmi zuwa

[1] **Kashful Asrar** na Musawi, shafi na 91-92.

Karbala. Malaminsu Majalisi ya ruwaito kamar haka: "Lallai Mahadi zai rushe Masallaci mai Alfarma har sai ya mayar da shi ga harsashensa. Kuma zai rushe Masallacin Annabi zuwa harsashensa."[1] Har yau, a wani wurin dabam, Majalisi ya ruwaito kamar haka: "Farkon abinda zai fara da shi – yana nufin Mahadi – shi ne ya fitar da waɗan nan biyun (watau Abubakar da Umar daga kabarinsu) suna ɗanyu shataf (kamar yanzu aka bunne su) ya watse su a iska, sa'an nan ya rushe Masallacin."[2]

Ita Karbala da suke burin mayar da ita sabuwar alƙibla bayan rushe Ka'aba wuri ne kusa da birnin Kufa (a yanzu tana ƙasar Iraƙi) inda a nan ne aka kashe Sayyidina Hussaini ɗan Ali binu Abi Ɗalib, Allah ya ƙara musu yarda. A gwargwadon aƙidar Shi'a, kasancewar Hussaini ya yi shahada a wannan wuri shi ya ba wurin falala da ɗaukaka waɗanda Rafilawa suka yi ta kambamawa har daga ƙarshe suka fifita shi a kan garin Makka da Ɗakin Ka'aba. Daga ƙarerayin da suka laƙa wa wannan wuri domin su ƙawata shi ga jahilai, sun ce wai masallacin annabawa ne kuma za'a kawo dutsen Hajarul Aswadu wurin bayan rushe Ka'aba. Sun ruwaito ɗaya daga imamansu yana huɗuba, yana cewa: " Ya ku mutanen Kufa, lallai Allah mai girma da ɗaukaka ya ba ku abubuwan da bai ba wani ba na falala. Masallacinku shi ne ɗakin (Annabi) Adamu da (Annabi) Nuhu da (Annabi) Idrisu, kuma shi ne masallacin (Annabi) Ibrahimu… Kuma kwanuka ba za su tafi ba sai an kafa (dutsen) Hajarul Aswadu a cikin sa."[3]

Girmama Karbala da ɗaukan ta a matsayin ƙasa mai tsarki da fifita ta a kan Ka'aba ƙaryatawa ne ƙarara ga Alƙur'ani mai girma. Allah Maɗaukaki yana cewa:

---

[1] **Biharul Anwar** na Majalisi, mujalladi na 52 shafi na 338; kuma a duba **Kitabul Gaiba** na Abu Ja'afar Muhammad binul Hassan Aldusi, bugun Madabi'ul Nu'uman, ba garin bugu, ba tarihi, shafi na 282.
[2] **Biharul Anwar,** tushen da ya gabata, mujalladi na 52 shafi na 386.
[3] **Alwafi** na Faid Kashani, bugun Almaktabatul Islamiyya, Tehran-Iran, ba tarihi, mujalladi na 1 shafi na 215.

"Kuma lalle ne, Ɗaki na farko da aka aza domin mutane, haƙiƙa, shi ne wanda ke Bakka mai albarka kuma shiriya ga talikai." (Suratu Ali Imrana: 96).

Kuma masallacin Ibrahim wanda ya gina da umarnin Allah shi ne Ɗakin Ka'aba, kamar yadda Allah ya bayyana: "Kuma a lokacin da muka iyakance wa Ibrahim wurin Dakin (muka ce masa), "Kada ka haɗa kome da ni ga bauta, kuma ka tsarkake Ɗakina, domin masu ɗawafi da masu tsayuwa da masu ruku'u da masu sujada. Kuma ka yi yekuwa ga mutane da wajabcin Hajji, su je maka suna masu tafiya da ƙafafu da kuma a kan kowane maɗankwarin raƙumi masu zuwa daga kowane rango mai zurfi." (Suratul Hajji: 26-27). Kuma Ubangiji Maɗaukaki ya ce, "Kuma a lokacin da Ibrahim yake ɗaukaka harsashin gini ga Ɗakin, da Isma'ila (suna cewa), "Ya Ubangijinmu, ka karɓa daga gare mu, lalle ne kai, kai ne mai ji, mai sani." (Suratul Baƙara: 127).

Dangane da alƙibla kuwa, Allah Maɗaukaki yana cewa, "Lalle ne, muna ganin jujjuyawar fuskarka a cikin sama. To lalle ne, mu juyar da kai ga Alƙibla wadda kake yarda da ita. Sai ka juyar da fuskarka wajen Masallaci Tsararre." (Suratul Baƙara: 144). Watau Masallaci mai Alfarma, Ɗakin Ka'aba. Har yau, yana cewa, "Kuma daga inda ka fita, to, ka juyar da fuskarka a wajen Masallaci Tsararre, kuma inda kuke duka, to, ku juyar da fuskokinku a wajensa." (Baƙara: 150).

Wannan shi ne abinda Alƙur'ani mai tsarki yake faɗi dangane da ƙasa mai tsarki da kuma alƙiblar Musulmi wacce ba ta canjawa kuma ba ta sauyawa har abada. Daga wannan kuma babu wata ƙasa mai tsarki sai Baitil Maƙadis wanda Allah yake cewa dangane da shi: "Tsarki ya tabbata ga wanda ya yi tafiyar dare da bawansa da dare, daga Masallaci mai Alfarma zuwa ga Masallaci mafi nisa, wanda muka sanya albarka a gefensa." (Suratul Isra:1). Sai kuma Masallacin Annabi

(SAW) na Madina.  Waɗan nan su ne masallatai guda uku masu alfarma waɗanda ambatonsu ya zo a cikin hadisin da Manzo (SAW) yake cewa:  "Ba'a ɗaura sirada (domin tafiya) sai zuwa masallatai uku kawai:  Masallaci mai Alfarma, da Masallaci Mafi Nisa, da Masallacina wannan."[1]

Don haka Karbala ba ta da wata alfarma kuma ba ta da tsarki, sa'an nan babu bambanci tsakaninta da ko wace irin gama-garin ƙasa a duniya.  Muna roƙon Allah ya buɗe basirarmu tare da Shi'awa waɗanda ba su yi nisa ba.  Ya bayyana mana gaskiya ya ba mu ikon bin ta.  Waɗanda suka yi nisa kuma, Allah ya isar wa Musulunci sharrinsu.

Har yau, wani mugun nufi da Rafilawa suka daɗe da shi a zuci kuma suke da niyyar zartar da shi a aikace, shi ne kashe Musulmi Ahalus Sunna mafi munin kisa ta yadda ba abinda zai rage a cikinsu sai kaɗan.  Kasurgumin malamin 'yan Shi'a wanda suke yi wa laƙabi da *Shaikhul Ɗa'ifa*, watau Shaihin Kungiya, mai suna Abu Ja'afar Muhammad binu Hassan Alɗusi, ya ce, "Wannan al'amari (yana nufin mulkin 'yan Shi'a) ba zai tabbata ba sai ushuri tara na mutane sun tafi."[2]

Duba ka gani, malam mai karatu, wannan ƙeta da mugun nufi da baƙin alkaba'i da yake cikin zukatan malaman Shi'a da manyan mabiyansu.  Mulkinsu ba zai tabbata ba sai sun kashe ushuri tara na mutane, watau casa'in bisa ɗari ke nan (90%).

Ruwayar Majalisi ta fi ban tsoro da kaɗa zuciya da tsuma jiki.   Ga yadda ya hakaito daga imaminsu na shida, Abu  Abdullahi, wai ya ce, "Da mutane sun san abinda Mahadi zai yi idan ya bayyana da mafi yawansu sun yi fata kada su gan shi saboda yawan mutane da zai kashe…  Har mutane da yawa za su riƙa cewa:

[1] **Bukhari** da **Muslim.**
[2] Duba **Kitabul Gaiba** na Aldusi, tushen da ya gabata, shafi na 135.

Wannan ba ya cikin iyalin Muhammad; da yana cikin iyalin Muhammad da ya yi jin ƙai."[1]

Idan mai karatu yana so ya san su wane ne waɗan nan mutanen da wannan shu'umin Mahadi, Mahadin Yahudawa da Majusawa, zai kashe, to sai ya koma ga maganar Ayatullahi Khumaini da muka naƙalto a baya kaɗan inda ya sarraha da cewa Ahalus Sunna suke nufi. Muna fata Allah ya raba mu da ganin wannan baƙin Mahadi mai baƙar aniya da mugunyar manufa.

Har ila yau, wani mugun nufi da 'yan Shi'a suka daɗe da shi a zuci kuma suke da niyar tabbatar da shi a aikace, shi ne sauya addinin Musulunci da wani addinin sabo da sauya Shari'arsa da wata shari'a sabuwa da kuma sauya littafinsa da wani littafin sabo. Majalisi ya ambata a cikin littafinsa kamar haka: "Mahadi zai bayyana da al'amari sabo, da littafi sabo, da hukunci sabo."[2]

Idan kana da wani kokwanto dangane da wannan sabon al'amari, bari ka ji ruwayar Kulaini, wanda 'yan Shi'a suke ɗaukar sa kamar yadda Ahalus Sunna suka ɗauki Imamul Bukhari, daga Abu Abdullahi, imamin Rafilawa na shida, cewa wai ya ce: "Idan Mahadin iyalin Muhammadu ya bayyana, zai yi hukunci da hukuncin (Annabi) Dawud da (Annabi) Sulaiman kuma ba zai tambayi shaida ba."[3]

E, ba zai tambayi shaida ba; saboda tambayar shaida yana daga cikin sifofin Musulmi, shi kuwa wannan Mahadin Bani Isra'ila ne ya yafa mayafin iyalin Muhammadu (SAW), Ahlul Baiti, domin ɓad da bami. Saboda haka zai bar Shari'ar Annabi Muhammad (SAW), shugaban Ahalul Baiti, ya kama ta annabawan Bani Isra'ila.

---

[1] **Biharul Anwar** na Majalisi, tushen da ya shude, mujalladi na 52 shafi na 303.
[2] **Biharul Anwar,** tushen da ya shude, mujalladi na 52 shafi na 354.
[3] **Usulul Kafi** na Abu Ja'afar Muhammad binu Ya'aqub Alkulaini, ta'aliqin Ali Akabar Gifari, bugun Darul Kutubil Islamiyya, Teheran-Iran, ba tarihi, mujalladi na 1 shafi na 397.

Wannan shi ne mugun nufin ‘yan Shi’a ga al’ummar Musulmi kamar yadda yake a cikin littafan malamansu waɗanda suke izna da su. Kuma cewa wannan mugunyar manufa sai Mahadinsu ya bayyana za su zartar da ita, wata dabara ce ta koya wa mabiyansu juriya da haƙurin jira da dako. Gaskiyar lamari shi ne, duk lokacin da dama ta samu, ‘yan Shi’a suka kafa daula, ko suka samu ƙarfi, to wannan ne lokacin zartar da wannan manufa. Ba sai Mahadi ya bayyana ba.

Idan mai karatu yana son tabbatar da haka, sai ya koma ga maganar Imam Khumaini inda yake cewa, jim kaɗan bayan kafa Jumhuriyar Islama ta Iran, “Sayyid Hussain, lokaci ya yi na zartar da wasiyar imamai, amincin Allah ya tabbata a gare su. Za mu zubar da jinin nasibawa (Ahalus Sunna), mu karkashe ‘ya’yansu maza, mu raya matansu. Ba za mu bar ɗaya daga cikinsu ya kuɓuta ba daga wannan uƙuba. Da sannu dukiyoyinsu za su zama ganima ga Shi’ar Ahalul Baiti. Kuma za mu shafe Makka da Madina daga doron ƙasa saboda waɗan nan birane biyu sun zama mafakar ‘yan Wahhabiya. Kuma lallai ne Karbala, ƙasar Allah mai tsarki, ta zama ita ce alƙiblar mutane a cikin sallah. Za mu tabbatar da burin imamai, aminci ya tabbata a gare su,”[1] kamar yadda muka gani a baya kaɗan.

Bayan kafa Jumhuriyar Islama ta Iran, ‘yan Shi’a ba su jira zuwan Mahadi ba, amma sun ci gaba da zartar da mugun nufinsu ga al’umma, kamar yadda za mu gani a ƙarshen babi mai zuwa, in Allah ya yarda.

[1] **Kashful Asrar** na Musawi, shafi na 91-92.

**Babi na Biyu**

**Baƙin Tarihin 'Yan Shi'a**

'Yan Shi'a suna aiwatar da mugun nufinsu, wanda yake ƙunshe a cikin aƙidunsu kamar yadda muka gani, a duk lokacin da suka samu damar yin haka. Koda yake sun dangana yawancin miyagun manufofinsu da bayyanar Mahadi, amma tarihi ya tabbatar da cewa bayyanar Mahadi a wajensu shi ne kawai samun iko. A duk lokacin da 'yan Shi'a suka samu damar kafa daula, ko bayyanar wani shugabanci mai ƙarfi, to suna yin amfani da wannan don cimma manufofinsu. Don haka muke gani a yau, ƙasar Iran, bayan juyin juya halin Rafilawa, ta zama babban jigo na fitina da rashin zaman lafiya a ƙasashen Musulmi, musamman a Gabas ta Tsakiya.

A wannan babi na biyu, za mu gabatar da misalai na baƙin tarihin Shi'a a ƙasashe dabam-daban da lokuta dabam-daban.

## Kisan Shugabanni da ta da Fitinu

Kasancewar ƙungiyar Shi'a an kafa ta don yaƙar Musulunci daga ciki, mabiyan tafarkin Rafilanci sun ƙaddamar da ayyukan ta'addanci a kan Musulmi a tsawon tarihi. Wannan ya haɗa da kashe-kashe da zagon ƙasa ga marayar Musulmi da kafa ƙungiyoyin asiri iri-iri domin yaƙar Musulunci da rusa aƙidarsa. Wani salo na yaƙi da suka daɗe suna yin amfani da shi, shi ne kisan shugabanni

Ba 'yan Shi'a ne suka fari kisan shugabanni ba a tarihin bil Adama, amma sun ƙware a kansa, kuma sun shahara da shi. Wannan ya sa su Turawa daga wajen su ne suka samu kalmarsu ta **assassination,** wacce take nufin kisan shugabanni, kamar yadda za mu gani a nan gaba, in Allah ya yarda.

Abu ne da aka sani cewa shugabanni su ne kai ga ko wacce al'umma, kuma kamar yadda jiki ba shi da amfani idan babu kai, to haka al'umma idan ba ta da shugabanci. Wannan ya sa 'yan Shi'a, a matsayinsu na rantsattsun masu gaba da Musulunci, suka mayar da kisan shugabannin Musulmi sana'a wacce suka shahara da ita

Shugaba na farko da suka kashe a tarihin Musulunci shi ne Sarkin Musulmi Umar binul Khaɗɗabi, Allah ya ƙara masa yarda. Abu Lu'ulu'atal Majusi ne ya kashe shi domin rama gayya ga rushe daular Farisa ta Majusawan Iran da khalifan ya yi. Abu Lu'ulu'ata Bamajuse ne da aka ribato shi a wajen yaƙi, kuma ya zama bawan Sahabin Annabi, Mugira binu Shu'uba, Allah ya ƙara masa yarda, yana zaune tare da shi a Madina. Ya shiga sahun sallah a Masallacin Annabi(SAW) da asuba, ya soki Umar da wata wuƙa mai baki biyu wacce ya sa mata dafi, a lokacin da Umar yake limancin mutane a cikin sallah. Sa'an nan ya yi ta sukan masallata dama da hagu sai da ya soki mutum goma sha uku, waɗanda bakwai daga cikinsu suka yi shahada.

Saboda wannan aika-aika da ya yi, 'yan Shi'a na ko wane zamani suna ɗaukar Abu Lu'ulu'ata a matsayin gwarzo, kuma suna yi masa laƙabi da **Baba Shuja'uddin,** watau Baba Sadaukin Addini! Gwamnatin Musulunci (wai ma!) ta ƙasar Iran ta gina masa **Hubbare** a birnin Kashana dake tsakiyar ƙasar. Wannan Hubbare da ta ƙunshi makeken gini mai babbar ƙofa, ma'abota jahilci suna ziyarar ta daga ko ina a duniya domin tunawa da Bamajuse Abu Lu'ulu'ata da babban aikin da ya gabatar na kashe Khalifa Umar! Har yau, gwamnatin ƙasar Iran ta sanya hoton wannan **Hubbaren** a kan irin katin nan na aikewa da saƙo (postcard) da kuma kan-sakri na aike wasiƙu (stamp) don a yaɗa ta kuma a jawo hankalin masu ziyara, da masu yawon buɗe idanu, zuwa gare ta.[1]

Mai son ya ga hoton Hubbaren Abu Lu'ulu'ata sai ya shiga sashen **Google** na yanar gizo, ya sanya sunan "Abu Lu'ulu'ah" ko "Fairuz" sa'an nan ya latsa. Zai ga abin mamaki. Mai karatu, me zai hana ka gwada don ka gane wa idanunka!

Shugaba na biyu da Rafilawa suka kashe shi ne Sarkin Musulmi Usmanu binu Affan, Allah ya ƙara masa yarda. Abdullahi binu Saba'i Bayahude, wanda ya aza tubalin farko na ginin tafarkin Shi'anci, shi ya fari fitinar da ta kai ga kisan sa.

[1] A duba **Kashful Asrari** na Musawi, tushen da ya shude, shafi na 88.

Kashe-kashen Rafilawa ga shugabannin Musulunci bai tsaya a kan Sahabbai da magabatan Ahalus Sunna ba kawai, a'a ya haɗa har da imaman Shi'a da shugabannin Ahalul Baiti. Mafi shahara a cikinsu shi ne Imam Hussaini, Allah ya ƙara masa yarda, wanda mabiyansa 'yan Shi'a ne suka yi sanadin mutuwarsa.[1] Haka nan, su suka yi sanadin mutuwar Imaminsu na bakwai, Imam Musa Alkazim, kamar yadda su da kansu suka tabbatar.[2]

A taƙaice kisan shugabanni, ko kuma abinda ake kira da Turanci **assassination**, ya zama wata hanya ta yaƙar Musulunci wacce Rafilawa suke amfani da ita a ko wane zamani. A nan kusa-kusa sun kashe manyan malamai kamar su Muhammad Hussaini Azzahabi mai littafin **Attafsiru wal Mufassirun** da Ihsan Ilahi Zahir sanannen marubuci ɗan ƙasar Pakistan wanda ya shahara da rubutu a kan 'yan Shi'a. Kamar yadda suke kashe duk wani malaminsu da ya tuba ya koma Sunna irin su Sayyid Ahmad Kasarawi da Dr Musa Musawi wanda ya rubuta littafin **A Critical Revision of Shi'ah** yana kira da a yi gyara a tafarkin Shi'anci.

A nan Nijeriya, a cikin 'yan shekaru kaɗan da suka gabata, 'yan Shi'a sun kashe malamai, na ƙarshensu Malam Umaru Ɗan Maishiya wanda suka kashe a Sakkwato. Wataƙila ba zai zama adalci ba idan muka dangana wa 'yan Shi'a kisan Malam Ja'afar kai tsaye; saboda shi yana da maƙiya masu yawa. Amma muna iya dangana musu kisan Malam Umar Ɗan Mai Shiyya saboda shi ba shi da abokan gaba sai 'yan Shi'a.

Kuma ina cikin gyaran wannan littafi don miƙa shi ga masu bugu, sai aka ƙara tafka ta'asar kisan gilla ga Malam Muhammad Auwal Adam Albani a ranar Asabar 1 ga watan Rabi'ul Thani, 1435/ 1 ga Fabrairu, 2014. Muna roƙon Allah Maɗaukaki ya karɓe shi a cikin masu shahada waɗanda suka bi turbar annabawa da magabata na-gari.

"Ya Ubangijinmu, ka yi gafara gare mu, kuma ga 'yan uwanmu waɗanda suka riga mu yin imani, kada ka sanya ƙulli a cikin zukatanmu ga waɗanda suka yi imani. Ya Ubangijinmu, lalle kai mai tausayi ne, mai jinƙai."(Suratul Hashri: 10).

---

[1] Duba littafinmu, **Wa Ya Kashe Hussaini?** bugun Zomo Press, Kaduna, 2010, shafi na 7-18.
[2] Duba **Rijalul Kasshi** na Muhammad binu Umar Alkasshi dan Shi'a, shafi na 229.

Shaihu Ali Muhammad Sallabi ya zana wani kwami da sunayen shugabannin Musulunci waɗanda ‘yan Shi’a suka kashe a zamuna dabam-daban, da ƙasashe dabam-daban, a ƙarshen litafinsa mai suna **Daulatus Salajiƙah**. Kwamin ya ƙunshi sunayen fitattun shugabanni 42 waɗanda suka haɗa da khalifofi da sarakuna da alƙalai da kwamandojin soji da manyan malamai da attajirai.[1]

Imam Suyuɗi ma ya zana sunayen shugabannin Musulmi da ‘yan Shi’a suka yi wa kisan gilla a cikin littafinsa, **Tarikhul Khulafa**.

Abinda wannan yake nunawa shi ne cewa, ‘yan Shi’a an san su da sana’ar kisan shugabannin Musulmi waɗanda ba sa bin tafarkinsu, musamman Ahalus Sunna waɗanda suke ganin jininsu ya halatta.[2]

## Haddasa Fitina A Tsakanin Musulmi

Rafilawa suna ɗaukar haddasa fitina tsakanin Musulmi a matsayin wata hanya ta yaƙar Musulunci da ƙoƙarin rusa shi. Kuma wannan abu ne da suka shahara da shi a tsawon tarihi. Fitina ta farko da suka haddasa ita ce tawayen da aka yi wa Sarkin Musulmi Usmanu binu Affan(RA) wanda ya ƙare da kisansa kisan gilla, kuma ya haifar da faruwar saɓani a tsakanin al’umma wanda ya kai ga yaƙoƙa masu yawa. Yaƙin Jamal da yaƙin Siffain da yaƙin Nahrawan, da wasu gomomi da ɗaruruwan yaƙoƙa da suka biyo bayan waɗan nan, duka sakamakon fitinar Abdullahi binu Saba’i ce wanda ya assasa tafarkin Shi’a.

Wani salon fitina da ‘yan Shi’a suka shahara da shi, shi ne taimakon kafirai a kan Musulmi koda yaushe yaƙi ya tashi a tsakanin ɓangarorin biyu. Misalan irin wannan aiki nasu ba za su ƙidayu ba, amma wanda ya fi shahara a tarihi shi ne yaƙin Tattar a kan Bagadaza.[3] A wannan zamani da muke ciki ya tabbata cewa Rafilawan Iran sun taimaka wa Amurkawa da sauran kafiran Turai a kan yaƙin Afganistan da Iraƙi, banda samar da makamai da horon soji ga ƙungiyoyin Shi’a ‘yan ina-da-kisa na Iraƙi waɗanda suke karkashe Ahalus Sunna na ƙasar. Waɗan nan duka abubuwa ne waɗanda suke an tabbatar da su ta hanyar bincike na zahiri,

---

[1] Duba **Daulatus Salajiqah** na Sallabi, bugun Darul Ma’arifa, Bairut, 1430/2009, shafi na 654-656.

[2] Domin ganin fatawoyin malaman Shi’a da nassoshin imamansu da suke nuna halaccin jinin Musulmi a addinin Shi’a, sai a duba littafinmu, **Matsayin Musulmi a wajen ‘Yan Shi’a**.

[3] Za mu fayyace bayani a kan wannan a nan gaba kadan, in Allah ya yarda.

kuma bayanansu suna nan a cikin kundayen bincike na hukumomi da ƙungiyoyi daban-dabam.

## Kafa Kungiyoyin Asiri

Wani salon ta'addanci da 'yan Shi'a suka ɗauka don yaƙar Musulunci shi ne kafa ƙungiyoyin asiri domin yaɗa hayaniya da dambarwa da ɓata aƙidojin Musulunci da hana zaman lafiya a marayar Musulmi. Baƙin tarihin Shi'a yana cike da irin waɗan nan ƙungiyoyi.

Wataƙila mafi daɗewa kuma mafi sharrin waɗan nan ƙungiyoyi ita ce ƙungiyar Isma'iliyya. 'Yan wannan ƙungiya suna dangana kansu ga Isma'il binu Ja'afar Sadiƙ, ɗan imamin Shi'a na shida, kuma sun yi ƙaurin suna da yawan tashin-tashinar siyasa, tawaye da bore da kisan shugabanni. Bayan sun yi tawaye ga imamin Shi'a na bakwai, Musa binu Ja'afar Sadiƙ, sun goyi bayan ɗan uwansa Isma'il, shi ma sun ya da shi suka koma ga Almusta'ali Billah, khalifan Faɗimawa 'yan Shi'a na tara a Misira, wanda shi ma suka yi masa tawaye ƙarƙashin jagorancin shaƙiƙinsa, Nizar binu Ma'ad, suka kafa wata 'yar ƙaramar daula a garin Iskandariyya na Masar.

A shekarar 1090 miladiyya, wannan 'yar daula tasu ta rushe, sai suka yi ƙaura ƙarƙashin jagorancin shugabansu, Hassan binul Sabbah, zuwa lardin Almautu na ƙasar Iran inda suka kafa ƙungiyar ta'addanci ta Hasshashun. Wannan suna nasu an samo shi daga kalmar **hashish** wacce take nufin ganye, watau wiwi, wanda ake sha don buguwa.

A wannan lokaci ne Isma'iliyya suka kai ƙololuwar ta'addancinsu, inda suka bazu a dazuka da kan duwatsu, suna tare hanya, su kashe maza, su kame mata da yara, su kora dabbobi waɗanda suke gasawa su ci bayan sun yi maye. Idan wani sarki ko hakimi ko mai mulki ya yi ƙoƙarin magance ta'addancinsu, sai su aike wanda zai yi shigar burtu ya kashe shi kisan gilla. Daga nan sunan **hasshashun** ya yi dai-dai da masu kisan shugabanni, wanda Turawa suka ara suka mayar **assassins.** Wannan sai ya zama wani abin "alfahari" a cikin baƙin tarihin 'yan Shi'a cewa su ne suka koya wa Turawa, sarakan kisa, yadda ake kashe shugabanni!

A wannan zamani namu, ƙungiyar Isma'iliyya ta rikiɗe, ta fito da sunan Agha Khan Foundation, inda take gina makarantu da asibitoci, tana da'awar taimakon Musulmi marasa galihu, amma manufarta ita ce juye kansu da ɓata aƙidarsu. Turawa 'yan mishan sun rungumi wannan ƙungiya (hedukwatarta tana London) kamar yadda suka rungumi ƙungiyar Ahmadiyya, saboda manufarsu ɗaya ce.

Cibiyar Agha Khan tana gudanar da nashaɗinta yawanci a gabashin Afrika. Na gani da idona irin makarantu da asibitoci da take ginawa a ƙasashen Uganda da Kenya da Tanzaniya. A ɓangarenta na Turai kuwa, cibiyar tana lulluɓe ayyukanta da mayafin bincike na ilmi da kimiyya, kamar yadda cibiyoyin Yahudawa masu miyagun manufofi suke yi. A shekarar 2011, wannan ɓangare na ƙungiyar ya bai wa sarkin Masarautar Kaɗar dake Tekun Fasha "Lambar Yabo ta Inganta Gine-ginen Musulunci Masu Tarihi." Wannan wata hanya ce da ƙungiyoyin ta'addanci (irin ta'addancin da kafiran Turai suke maraba da shi) suke sa wa kawunansu rigar mutunci, kuma kafafen labarai na duniya su riƙa kambama su, don su ji daɗin zambatar gafalallu.

Banda ta'addanci na kashe-kashe, ƙungiyar Isma'iliyya ta ƙaddamar da ta'addancin aƙida kuma, inda ta shigo da miyagun aƙidu na Maguzanci cikin wasu ƙungiyoyin Musulmi. Aƙidar **Faila** ta 'yan Tijjaniyya, ko kuma mu ce 'yan Inyasiyya, tana cikin irin waɗan nan aƙidu.[1]

Wata ƙungiyar ta'addanci da Rafilawa suka kafa ita ce ƙungiyar Karmaɗiyya. Wanda ya kafa wannan ƙungiya shi ne Karmaɗ Hamdan. Asalinsa daga lardin Khuzistan na ƙasar Iran yake, ya ɓalle daga ƙungiyar Isma'iliyya, kuma ya yi ƙaura zuwa Kufa a Iraƙi inda ya kafa tasa ƙungiyar. Yawancin ta'addancin Karmaɗiyya na aƙida ne. Ita ce ta ɗauki tutar yaɗa aƙidar Baɗiniyya wacce take koyar da cewa Alƙur'ani yana da ma'ana biyu: ta ɓoye da ta sarari, kuma babu wanda ya san ta ɓoyen daga imaman Shi'a sai gausayen Ɗariƙa.[2]

Addinin Baha'iyya shi ma ya samo asali daga aikin ta'addancin aƙida na 'yan Shi'a. Wanda ya kafa wannan addini shi ne Baha'ulla, wanda ya rayu tsakanin

---

[1] Domin ganin dangantakar akidun Shi'a da Darika sai a duba **Muqaddimatu Ibni Khaldun** na Abdurrahman binu Khaldun, bugun Darul Kutubil Ilmiyya, Bairut, 2003, shafi na 254 da 386. Kuma domin darasun tushen akidar **Faila** a cikin kungiyar Isma'iliyya, sai a duba **Altuhfatus Saniyya** na Dr Tahir Maigari, shafi na 133. Na fassara wannan littafin zuwa harshen Hausa da taken **Jana'izar Tijjaniyya.** Littafin ya fito a shekarar 2015; nemi kwafenka.
[2] Domin karin bayani, duba littafinmu **Bankaurar Sufaye.**

shekarun 1817 zuwa 1892. An haife shi a birnin Teheran na Iran, kuma ya rasu a garin Akka a kan gaɓar kogin Bahar Maliya. Asalin Baha'ulla ɗan Isma'iliyya ne, amma daga bisani ya yi shelar kafa sabon addini mai zaman kansa. Aƙidojin wannan addinin da ibadojinsa gamin-gambiza ne na aƙidun Musulunci da Kiristanci da tsoffin addinan Gabas Mai Nisa, kamar Budanci da Barhamanci da Komfusanci da sauransu. Suna gina ɗakin ibada a kewaye kamar rumbu, babu mihirabi ko alƙibla, saboda su sama suke kallo idan suna sallah.

Turawan mulkin-mallaka suna yabon Baha'iyyanci saboda, a faɗinsu, yana da sassauci kuma ya tattare alheran dake cikin dukkan addinai!! Yahudawa ma suna tallan wannan addinin, suna taimaka masa da dukiya, saboda ya dace da manufarsu ta yaƙar Musulunci. A yau, hedukwatarsa ta duniya tana can a kan dutsen Mount Carmel dake bayan garin Haifa a Isra'ila.

Durzawa, ko kuma Duruz, wata tsohuwar ƙungiyar ta'addanci ce da 'yan Shi'a suka kafa. Ta shahara da yin biyayya ga khalifan Faɗimawa 'yan Shi'a na shida, Alhakim bi Amrillah, wanda ya yi mulkin Misira tsakanin shekarun 996 zuwa 1021 miladiyya. Bayan raunin daular Faɗimawa, Durzawa sun zauni duwatsun Lebanon inda suka mayar ƙasarsu har zuwa yau. Sun taimaka wa Yahudawan Isra'ila a kisan ƙare-dangin da suka ƙaddamar a kan Falasɗinawa a Lebanon a shekarar 1982, kuma a yau su ne ƙashin bayan ƙungiyar ta'addanci ta Hizbullah wacce Hassan Nasarallah yake jagoranta. Kungiyar Hizbullah 'yan Shi'ar Nijeriya ƙarƙashin jagorancin Zakzaki suna da alaƙa ta ƙut-da-ƙut da ita. Har ma idan suka fito jerin gwanonsuna Maulidi, wanda wasu 'yan ɗariƙa da Kiristoci suke taimaka musu, sukan ɗaga tutocin ƙungiyar don bayyana wannan alaƙar a fili.[1]

Wani abu da bai kamata mu wuce ba tare da mun ambace shi ba, shi ne cewa ɓurɓushin Durzawa suna nan a cikin mutanen nan da muke kira Kwarori waɗanda suke zaune a Nijeriya, musamman a biranen Kano da Ikko. Kuma koda yake suna kauwame kansu, ba sa gauraya da mutane ta hanyar auratayya ko mu'amala, amma babu laifi mu yi gargaɗi da cewa suna ɗauke da aƙidar Shi'a kuma suna taimakawa wajen yaɗa ta a fakaice.

---

[1] Duba hoton 'yan Shi'a suna dauke da tutocin Hizbullah a jaridar **Daily Trust**, fitowar Talata, 22 ga watan Mayu, 2012, shafi na 3.

## Taimakon Kafirai wajen Yaƙar Musulmi

Daga cikin abinda ‘yan Shi’a suka shahara da shi a baƙin tarihinsu akwai taimakon kafirai a wajen yaƙar Musulmi, da cin ƙasashensu, da take haƙƙoƙinsu, da zubar da jininsu, da keta alfarmarsu. Wannan ƙaramin littafi ba zai iya tattare abinda ya faru ba a wannan fanni, amma za mu ba da misali guda kawai.

A wajejen ƙarshen daular Abbasiya a ƙarni na bakwai bayan hijira, an yi wani sarki Mushriki mai suna Holako, sarkin Tattar. Wannan sarki ya yaƙi daular Musulmi mai faɗi, ya riƙa cin gari bayan gari. Duk garin da ya ci yana rushe shi baki ɗaya, ya kashe mazauna garin, ya ƙone gidaje da gonaki da dabbobi, ba ya barin kome. Saboda tsananin ɓarnar waɗan nan kafirai, har wasu mutane a zamanin sun zaci ko yajuju da majuju ne suka bayyana. Amma duk da haka, babban birnin daular Musulmi, watau Bagadaza, tana yi wa wannan sarkin kwarjini saboda girmanta da yawan mutanen dake cikinta da kuma ƙarfin sojan dake tsaron ta. A wannan lokaci, duk duniya babu birni kamar Bagadaza. Don haka da ya iso ƙasar Farisa sai ya tsaya yana tararrabi, yana shawara ya kawo wa Bagadaza hari ko a’a.

A wannan lokaci Sarkin Musulmi shi ne Musta’asim, Khalifa na ƙarshe a daular Abbasiya. Babban wazirinsa mai suna Muhammad binu Ahmad binu Alƙami ɗan Shi’a ne amma masu mulki sai suka yi sakaci da shi tun yana saurayi, ya yi ta hawa muƙamai har ya kai matsayin waziri. Saboda iya munafunci da amfani da taƙiya, Binu Alƙami ya samu amincewar kowa a wannan daula. Amma duk tsawon shekaru, shi dama yake jira ta rusa daular. Sai zuwan Holako da rundunarsa ya ba shi wannan damar.

Binu Alƙami ya aike wa Holako da bayanan sirri a ɓoye, ya yi bayanin raunin daular kuma ya yi alƙawarin taimakon maharan da sharaɗin cewa za su kafa

daular Shi’a bayan sun kawar da Khilafar Abbasiya. Lokacin da rundunar Tattar suka iso Bagadaza suka kafa sansani a bayan gari, Khalifa Musta’asim ya tsorata ainun, amma sai wazirinsa ya kwantar masa da hankali kuma ya nemi izini ya fita zuwa sansanin abokan gaba domin neman sulhu da su. Bayan ya je ya ƙara tabbatar da yarjejeniyarsa ta sirri da Holako, sai ya komo wajen sarkin Musulmi da wata ƙarya. Ya ce Holako ya yi farin ciki da zuwansa, ya amince da sulhu da barin yaƙi kuma har ma yana son ya aurar da ɗiyarsa ga ɗan sarkin Musulmi, Yarima mai jiran gado Abubakar. Sarki ya yi murna, aka sa ranar da za a je ɗaurin aure kuma daula duka ta fita zuwa sansanin Holako domin yin shagali.

Babu wanda aka bari a baya, Sarki da Yarima da manyan wazirai da kwamandojin soja da malamai da limamai da alƙalai da attajirai da duk wani mai faɗi a ji sun fita baki ɗaya. Isarsu sansanin Holako ke da wuya, da ma ya shirya. Sai ya sa aka kange mafita duka aka yanke shugabannin nan baki ɗaya, sai abokinsu waziri Binu Alƙami kawai ya rage. A yammaci guda sai Bagadaza, da sauran al’umma, suka zama jiki ba kai.

Su kuwa yajuju da majuju suka shiga aiki. Kwana arba’in suna kisa, suna ƙone gidaje da kasuwanni da masallatai da makarantu da ɗakunan karatu (laburare) sai da kogin Dajla ya rikiɗe ya zama ja saboda jini. Suka kame mata da yara, suka yi ta zina da mata sharifai Hashimawa a cikin masallatai.

Wannan shi ya kawo ƙarshen daular Abbasiya wacce ta yi shugabancin duniya ɗaruruwan shekaru kuma daga nan Musulmi ba su sake samun wannan matsayi ba na shugabancin duniya. Mutum miliyan ɗaya da dubu ɗari takwas

(1,800,000) ne suka rasa rayukansu a wan nan kisan kiyashi wanda tarihi bai taɓa ganin irinsa ba.[1]

Marubucin tarihi ɗan Shi'a mai suna Mirza Muhammad Baƙir Khuwansari, ya kawo wannan ƙissa a cikin littafinsa, *Raulatul Jannat,* yana yabon Waziri Binu Alƙami a kan wannan ɗanyen aiki da ya tafka, kuma ya ce waɗanda suka rasa rayukansu duka suna cikin wutar Jahannama.[2] Ayatullahi Khumaini ma ya yaba wa wannan ɗan ta'adda, maci amana, kuma ya ɗauki wannan mummunan aiki nasa a matsayin babbar hidima ga Musulunci!! Don haka ba ya ambaton sa sai ya ce: **Raliyallahu Anhu,** watau Allah ya yarda da shi![3]

Wannan yana nuna cewa ƙissar ba ƙage aka yi wa 'yan Shi'a ba; su ma sun san da ita, sun yi na'am da ita, kuma sun tabbatar da ita a cikin littafansu.

## Karyar Gwagwarmaya ta Kare

Yawancin 'yan Shi'ar Nijeriya an yaudare su zuwa shiga ƙungiyar da sunan GWAGWARMAYA. An nuna musu cewa juyin juya halin ƙasar Iran na shekarar 1979 juyi ne na Musulunci, kuma manufarsa ita ce ƙwato haƙƙin Musulmi da yaƙar zalunci da tabbatar da adalci.

Malam Ibrahim Zakzaki da maƙarrabansa, tare da wasu 'yan boko da wasu malaman addini masu jimirin sauyi, duka an yaudare su da wannan farfaganda. Sai suka ɗauki ƙasar Iran a matsayin wata jarumar ƙasa mai bajinta, wacce ta fito

[1] Domin ganin wannan kissa, sai a duba **Albidaya wal Nihaya** na Abul Fida Isma'il binu Kathir, bugun Darul Kutubil Ilmiyya, Bairut, 1408/1988, mujalladi na 9 shafi na 154; da **Almuntaqa min Minhajil I'itidal** na Muhammad binu Uthman Alzahabi, ta'aliqin Muhibbuddin Alkhadib, bugun Maktabatu Daril Bayan, ba tarihi, shafi na 298.

[2] Duba **Raulatul Jannat fi Ahwalil Ulama'i was Sadat** na Muhammad Baqir Alkhuwansari, bugun Bairut, 1991, shafi na 578.

[3] Duba **Kashful Asrar** na Sayyid Hussain Musawi, tushen da ya shude, shafi na 90.

domin yaƙar ƙasar Yahudu ta Isra'ila da uwargijiyarta Amurka. Ta haka ne, kuma sannu a hankali, da yawa daga cikin waɗan nan mutane suka shiga Shi'a ba tare da sani ba.

A yau, bayan kimanin shekaru 35 da juyin juya halin na Iran, mahukuntan ƙasar 'yan Shi'a sun yaye mayafin yaudara da ***taƙiyya,*** kuma sun fito fili suna nuna mugun nufinsu na yaƙar Sunna da yaɗa mugunyar aƙidarsu ta Shi'a. A yau tarihi yana maimaita kansa, inda ta'addancin 'yan Shi'a ya fito fili kuma ƙiyayyarsu ga wannan al'umma ta bayyana a sarari. Kasar Iran da masu goyon bayanta a ko ina a duniya su ke kan gaba wajen yaƙar Ahalus Sunna da zubar da jininsu da taimakon kafirai a kansu.

A nan za mu ba da misalai kaɗan na irin wannan ta'addanci don masu hankali su lura. Amma bari mu fara da bayanin rayuwar Ahalus Sunna a ƙasar Iran bayan juyin juya halin 'yan Shi'a.

## Rayuwar Ahalus Sunna A Kasar Iran

Mutane da dama ba su da masaniya cewa akwai Ahalus Sunna masu yawa dake rayuwa a ƙasar Iran saboda rashin jin ɗuriyarsu. Wannan kuwa ya faru ne a dalilin danniya da take haƙƙi wanda gwamnatin Iran ta Shi'awa take yi musu.

Bayan samun nasarar juyin juya halin Iran, shugabannin Shi'a sun fara da zartar da mugun nufin su a kan Ahalus Sunna na ƙasar, kafin su mayar da hankalinsu ga sauran Musulmi na wasu ƙasashe. Bayanai da alƙaluma masu biyowa, waɗanda suka fito daga kafafen gwamnatin Iran ita da kanta, suna tabbatar da haka.

A gwargwadon ƙididdigar san-san ta shekarar 2008, adadin mutanen Iran ya kai miliyan sittin da biyar, da dubu ɗari takwas da saba'in da biyar, da ɗari biyu da ishirin da uku (65,875,223). A cikin wannan adadi, kimanin miliyan 20 Ahalus Sunna ne. Gamin gambizar addinan ƙasar ya kasance kamar haka: Rafilawa: 65%, Ahalus Sunna: 25%, Yahudawa da Kirista da Majusawa: 10%. Yawancin Ahalus Sunna na ƙasar sun kasu izuwa ƙabilun Kurdawa da Balushawa da Turkumawa. Akwai Larabawa kaɗan a yankin ƙasar da ake kira Arabistan. Amma yawancin 'yan Shi'a su Farisawa ne.

Tun kafin juyin juya halin Iran, Ahalus Sunna, kasancewarsu ba Farisawa ba, sun fuskanci danniya da take haƙƙi. Wannan ya sa wasu daga cikin su suka goyi bayan juyin da fatan za su samu sa'ida, amma bayan cin nasara sai Khumaini ya juya musu baya har suka ƙwammace gidan jiya. Yawancin shugabannin Ahalus Sunna da suka marawa juyin baya, kamar su Shaihu Ahmad Mufti Zadah, Imam Khumaini ya sa an rataye su.

Duk da yawan Ahalus Sunna (kimanin rubu'in 'yan ƙasa), kundin tsarin mulkin ƙasar bai san da su ba. Maimakon haka, kundin ya bayyana ƙarara cewa ƙasar tana bin tafarkin Shi'awa 'Yan Dozin. A majalisar ƙasar mai wakilai 290, Ahalus Sunna kujeru 12 kawai aka ba su. Wannan yana nufin cewa, ko wane ɗan majalisa ɗaya Ahalus Sunna yana wakiltar kimanin mutane miliyan ɗaya da rabi ke nan, a yayin da ko wane wakili ɗan Shi'a yake wakiltar Shi'awa 200,000 kacal. Zaluncin wannan tsari ba sai an faɗi ba. A haƙiƙa ma, waɗannan kujeru 12 an bayar da su ne kawai saboda a yi talla da cewa an bayar; idan ba haka ba me 12 za ta yi a cikin 290?

Babu 'yancin addini ga Ahalus Sunna na Iran. An haramta musu gina masallatai a manyan biranen ƙasar, kamar Asfahan da Shiraz da Yazd. A babban

birnin ƙasar, Tehran, inda ake da Musulmi Ahalus Sunna miliyan guda, an haramta musu gina masallaci koda guda ɗaya, a yayin da aka ƙyale Yahudawa da Kirista da Majusawa suka gina wuraren ibada ɗai-ɗai ko wannensu. Masallatan Ahalus Sunna da aka ba su damar ginawa a ƙauyuka da yankunan karkara suna ƙarƙashin kulawar hukuma ta dun-dun-dun. Haka nan kuma an haramta musu kafa makarantu na kansu.

A taƙaice, Ahalus Sunna a Iran an haramta musu kafatanin haƙƙoƙinsu na 'yan ƙasa. A yau, su suka fi kowa ci baya da jahilci da talauci da rashin aikin yi a ƙasar.[1]

## Tarihi Yana Maimaita Kansa

Bayan gwamnatin juyin juya hali ta Iran ta shimfiɗa tsarin danne Ahalus Sunna a cikin gida, kuma a lokaci guda ta girke na'urar farfaganda domin farauto na waje, sai ta shiga ƙaddamar da aikin Shi'a na tarihi: yaƙar Musulunci da rushe tafarkin Sunna.

Kuma da yake a yanzu kiɗa ya sauya, to sai rawa ma ta sauya. Don haka a ci gaba da wannan yaƙi na tarihi, ƙasar Iran a matsayinta na mai riƙe da kambin yaɗa tafarkin Shi'a a duniya a yau, ta fara da ware dukiya mai yawa, wasu rahotanni suna faɗin kimanin kashi goma bisa ɗari (10 %) na dukkan dukiyar ƙasar, don wannan manufa. (Kada a mance Iran tana cikin ƙasashe huɗu da suka fi yawan arziƙin man petur a duniya.) Ta kafa cibiyoyi na ƙasa da ƙasa, kuma ta buɗe sassa a dukkanin ofisoshin jakadancinta dake ƙasashen ƙetare don tabbatar da wannan aiki.

[1] Alkaluman da muka bayar a sama sun fito daga Kamfanin Dillancin Labarai na Iran, IRNA. Dangane da sauran bayanai kuma, sai a duba littafin **Alshi'atu Shahidina Ala Anfusihim** na Liya'uddin Alkashif, bugun Maktabatu Ahlil Bait, 1428/2007; da littafin **Ahawalu Ahalis Sunna fi Iran** na Abdulhaqq Al'asfahani.

Sa'an nan ƙasar Iran ta kafa ƙawance da 'yan Shi'a na sauran ƙasashe, waɗanda ta zama uwa a gare su, su kuma suka zama 'ya'ya masu biyayya, saboda haɗa ƙarfi waje guda da samar da wani gagarumin yunƙuri don farfaɗo da yaƙin tarihi tsakanin Sunna da Shi'a wanda ya fara tun a zamanin Sahabbai, lokacin da aka rushe daular Farisa a ƙarƙashin jagorancin Sarkin Musulmi Umar binul Khaɗɗabi, Allah ya ƙara masa yarda.

Sabon yaƙin Shi'a a wannan zamani ya haɗe kafatanin fagage: fagen siyasa da diflomasiyya, fagen tattalin arziki, fagen ilmi da al'adu, da kuma fagen fama. Haka nan ya haɗe dukkan nau'in makamai: makamin kuɗi da abin duniya, makamin kafafen bayanai da yaɗa labaru, makamin **mutu'a** da **taƙiyya,** da makamin kisa wanda ya fara daga bindiga da bam har ya zuwa nukiliya.

## Sabon Ta'addancin Shi'a

A da, ƙasashen Turai da Amurka suna zargin Iran da cewa ita ƙasa ce ta 'yan ta'adda, mai ɗaurewa ta'addanci gindi, Musulmi na jin ciwo. Sai ga shi wannan zargi ya bayyana a zahiri, ta yadda duk mai idanu yake iya gani. Sai dai abin mamaki, a yanzu ƙasar Amurka tana maraba da ta'addacin Iran; saboda ta lura cewa yawancin ta'addancin nata a kan ƙasahen Musulmi mabiya Sunna yake ƙarewa. A yau, babu wata ƙasa a duniyar Musulmi wacce ta'addancin Iran bai addabe ta ba. Ga 'yan misalai:

Lebanon: Wannan ƙasa ita ce mazaunin ƙungiyar Hizbullah, ƙungiyar ta'addanci mafi ƙarfi a Gabas ta Tsakiya, wacce kuma ita ce hannun daman ƙasar Iran wanda take amfani da shi a wajen ayyukanta na ta'addanci a ƙasashen duniya.

Suriya ko Sham: Kasar Iran tana taimakon gwamnatin Bashar Asad ta tsuraru 'yan Shi'a wacce take kafsa yaƙi da 'yan tawaye masu bin tafarkin Sunna, waɗanda kuma su ne mafiya rinjaye, tun farkon shekarar 2011. Gwamnatin Asad ta dogara kacokan da taimakon Iran, na kuɗaɗe da makamai da diblomasiyya da ƙwararrun soji masu ba da shawara, wajen ta'addancinta a kan 'yan ƙasarta wanda ya haɗa da

rushe kimanin kashi biyu bisa uku na dukkan biranen ƙasar, kashe sama da mutane dubu ɗari biyu da hamsin, kore sama da miliyan shida daga gidajensu, da amfani da muggan makamai waɗanda aka haramta a dokokin ƙasa da ƙasa.

Yaman: Kasar Iran tana taimakon 'yan tawayen Hutsawa marasa rinjare, masu bin tafarkin Shi'a, a ƙoƙarinsu na ɓallewa daga ƙasar Yaman da kafa ƙasarsu ta 'yan Shi'a.

Iraƙi: Iran ta taimakawa 'yan Shi'ar Iraƙi wajen kafa ƙungiyoyin ina-da-kisa waɗanda suka taimaki sojojin Amurka a kan kifar da gwamnatin Saddam Hussaini da rushe biranen mabiya Sunna, kamar birnin Falluja, da karkashe su mafi munin kisa. A matsayin sakamako, ƙasar Amurka ta taimaka wa 'yan Shi'a su mulki ƙasar Iraƙi da da'awar cewa wai su ne masu rinjaye.

Baharain: Iran tana tallafawa 'yan Shi'ar ƙasar Baharain, waɗanda suke da'awar su ne masu rinjaye wai amma mabiyan Sunna suna mulkinsu mulkin danniya. Yau kimanin shekaru biyar ke nan babu zaman lafiya a ƙasar. Shekaru biyu da suka wuce, 'yan Shi'ar sun kusa yin nasarar tankwaɓe gwmnatin ƙasar ba don taimakon ƙasar Sa'udiyya ba gare su.

Nijeriya: A cikin watan Oktoba, 2010, jami'an tsaro sun kama kontena goma sha uku maƙare da miyagun makamai a tashar jiragen ruwa ta birnin Legas. Bincike ya tabbatar da cewa waɗan nan makamai sun fito ne daga ƙasar Iran, kuma ofishin jakadancin ƙasar a Abuja ya amsa cewa ɗaya daga mutanen da aka kama da makaman ma'aikacinsu ne. Bayan shari'a da ta ɗauki sama da shekaru biyu, an samu mutane biyu da laifi, ciki har da jami'in jakadancin na Iran, kuma kotu ta ɗaure su shekaru 17 ko wannensu.[1]

A cikin watan Fabrairy, 2013, jami'an leƙen asiri na Nijeriya sun cafke wasu samari da suka yi karatu a ƙasar Iran, suna shirin kai hare-haren ta'addanci da nufin kashe wasu shugabannin Musulmi na ƙasar nan, ciki har da tsohon shugaban mulkin soja Ibrahim Babangida, da Sarkin Musulmi mai murabus, Sultan Ibrahim Dasuƙi. Bayan bincike, ya tabbata cewa waɗan nan samari suna yi wa ƙungiyar

[1] Domin ganin wannan labari, duba jaridar **Dailay Trust,** fitowar 15 ga watan Mayu, 2013, shafi na 46.

ta'addanci da Iran ke mara wa baya, watau Hizbullah, aiki. Jaridun ƙasar nan da kafafen yaɗa labarai na ƙasashen ƙetare duka sun ruwaito wannan labari.[1]

Haka nan, a wannan shekara dai ta 2013, an gano makamai masu yawa ɓoye a wani gida a birnin Kano. Bayan bincike, an zargi wasu ƙwarori 'yan ƙasar Lebanon, waɗanda ake jin suna da alaƙa da ƙungiyar Hizbullah, da mallakar waɗan nan makaman.[2] Har yanzu maganar tana kotu.

Wannan ƙungiya ta Hizbullah, wacce take adana makamai a Kano saboda mugun nufi ga Musulmin ƙasar nan, 'yan Shi'ar Nijeriya ƙarƙashin jagorancin Ibrahim Alzakzaki suna ɗaga tutar ta a fili a cikin jerin gwano da suke gudanarwa a biranen ƙasar na.[3]

Abinda muka ambata a nan ɗan misali ne kawai na sabon ta'addancin 'yan Shi'a da uwargijiyarsu, ƙasar Iran, da kuma mugun nufi wanda suke ƙudure da shi ga wannan al'umma. Muna roƙon Allah ya tsare mu da sharrin bidi'a wacce take sunce imanin mutum ba da saninsa ba.

## *Muhimmiyar Sanarwa*

Dukkan littafan malaman Shi'a, da muka yi amfani da su a rubutun wannan taƙaitaccen littafi, akwai su a ɗakin karatu (laburare) na cibiyar **Markazus Sahabah** dake Sakkwato. Laburaren a buɗe take ga kowa da kowa.

*Tare da gaisuwar ɗan uwanku a Musulunci*

*Dr. Umar Labɗo*

---

[1] Gidan talabijin na **Aljazeera** (ta Larabci) ya watsa labarin ranar 21 ga watan Fabrairu, 2013.
[2] Duba jaridar **Dailay Trust,** Juma'a 31 ga watan Mayu, 2013, shafi na 1 da na 5.
[3] Domin ganin hoton 'yan Shi'ar Nijeriya dauke da tutocin Hizbullah, duba jaridar **Dailay Trust,** fitowar Talata 22 ga watan Mayu, 2012, shafi na 3.